WILL of GOD
316

# Ta Yaya Zan San Nufin Uba Maiduka?

*“Kada ku biye wa zamanin nan, amma ku bar halinku ya sāke, ta wurin sabunta hankalinku dungum, don ku tabbatar da abin da Allah yake so, wato nufinsa kyakkyawa, abin karɓa, cikakke kuma.”* Romawa 12:2

Sanin nufin Uba Maiduka da aikata shi yana da muhimmanci ƙwarai. Ku zama kamar Yesu. Ya ce ya zo duniya, *“ba domin in bi nufin kaina ba, sai dai nufin wanda ya aiko ni,”* Yahaya 6:38. Yawancin nufin Uba Maiduka yana shafar dukan masu bi a hanya ɗaya. Duk da haka, Uba Maiduka yana da nufi na musamman ga kowane mai bi, wanda yake bayyana masa a hankali yayin da yake girma cikin tafiyarsa da shi cikin aminci na yau da kullum. Za ka iya sanin nufin Uba Maiduka. Zai ba ka fahimta. *“Ka dogara ga Ubangiji da zuciya ɗaya, kada ka dogara ga abin da kake tsammani ka sani. A cikin dukan abin da kake yi, ka tuna da Ubangiji, shi kuma zai nuna maka hanyar da take daidai,”* Karin Magana 3:5-6. Kana sanin nufin Uba Maiduka na gaba ɗaya ga dukan masu bi daga Littafi Mai Tsarki. Kana sanin nufinsa na musamman ta hanyar haɗin Kalmar Uba Maiduka da rayuwa mai aminci da biyayya, ba tare da sabani ba. Daga wannan tushen biyayya, za ka iya gane nufinsa a gare ka kuma ka yi masa biyayya. Ka roki Uba. Ka nemi jagora daga Kalmarsa, hikimarsa, mutanensa, da salamar da yake bayarwa. Sa’ad da ka san nufin Uba Maiduka, ka yi masa biyayya.

**NUFIN UBA MAIDUKA NA GABA ƊAYA.** Mafi yawan nufin Uba Maiduka na gaba ɗaya yana cikin umarnai, ƙa’idoji, da misalan Littafi Mai Tsarki. Littafi Mai Tsarki shi ne babban tushen sanin nufin Uba Maiduka ga rayuwarka. *“Maganarka fitila ce wadda za ta bi da ni, Haske ne kuma a kan hanyata,”* Zabura 119:105.

1. Umarnai. Akwai umarnai da yawa a cikin Littafi Mai Tsarki ga dukan masu bi, kamar, *“Ku rika yin farin ciki a kullum. Ku rika yin addu’a ba fāsawa. Ku godiya ga Allah a kowane hali, domin shi ne nufin Allah a game da ku ta wurin Almasihu Yesu,”* 1 Tasalonikawa 5:16-18. Da kuma *“Gama wannan shi ne nufin Allah, wato ku yi zaman tsarki, ku guje wa fasikanci,”* 1 Tasalonikawa 4:3. Yesu ya ce, *“In dai kuna ƙaunata, za ku bi umarnina,”* Yahaya 14:15. Ka fahimci mahallin umarnan. Uba Maiduka ya gaya wa Nuhu ya gina jirgin ruwa, Farawa 6:14. Uba Maiduka bai gaya maka ka yi haka ba. Uba Maiduka ya gaya wa Dawuda ya tafi Hebron, 2 Sama’ila 2:1. Uba Maiduka bai gaya maka ka yi haka ba. Kada ka ɗauki umarni ka cire shi daga mahallinsa.

2. Ka’idoji. Akwai ƙa’idojin Littafi Mai Tsarki da ya kamata ka bi. Ka’idar kula da abin da aka ba mutum amana da kyau tana cikin Luka 16:1-13. Farashin zama almajiri yana ƙarshen Luka 14. Ka’idar neman waɗanda suka ɓata tana cikin misalai uku na Luka 15. Ka bi waɗannan da sauran ka’idojin da ke cikin Littafi Mai Tsarki.

3. Misalai. Umarnai da ƙa’idojin Littafi Mai Tsarki suna ba ka nufin Uba Maiduka na gaba ɗaya ga rayuwarka. Littafi Mai Tsarki yana ɗauke da misalai da za mu bi. Mafi kyawun misali shi ne rayuwar Yesu. Bayan ya wanke ƙafafun almajiransa, Yesu ya ce, *“Na yi muku ishara domin ku ma ku yi yadda na yi muku,”* Yahaya 13:15. Ya kamata mu bi misalinsa na tawali’u, Filibbiyawa 2:3-5. Ya kamata mu bi tafarkinsa, *“Domin a kan haka ne musamman aka kira ku. Gama Almasihu ma ya sha wuya dominku, ya bar muku gurbi ku bi hanyarsa,”* 1 Bitrus 2:21. *“Ta haka za mu san muna cikinsa: duk wanda ya ce yana zaune a cikinsa, ya kamata ya yi tafiya kamar yadda ya bi,”* 1 Yahaya 2:5-6.

**GARGAƊI.** Uba Maiduka ba ya yin karya, Zabura 119:160. Uba Maiduka ba zai jagorance ka ba, ko ya gaya maka, ka saba wa Kalmarsa ba. Yesu yana ba da shugabanni domin su shirya mu, Afisawa 4:11-14. Duk da haka, akwai malamai na ƙarya da yawa, 2 Timoti 4:3-4. Kada ka taba gaskata cewa Uba Maiduka yana gaya maka ka saɓa wa Kalmarsa. Uba Maiduka ba zai yi haka ba. Idan shugaban coci ya gaya maka ka saɓa wa Kalmar Uba Maiduka, wannan koyarwar karya ce.

**NUFIN UBA MAIDUKA NA MUSAMMAN.** Uba Maiduka yana da nufi na musamman ga masu bi, Zabura 32:8, Karin Magana 3:5-6. Ka yi biyayya ga nufin Uba Maiduka na gaba ɗaya. Sa'an nan, domin ka koyi nufinsa na musamman, ka roƙi Uba Maiduka da ƙwazo ya gaya maka. Ka nemi amsarsa daga Kalmarsa, hikimarsa, mutanensa, da salamar da yake bayarwa.

**Ka roƙa**. Ka yi addu'ar Dawuda, *"Ka koya mini in aikata nufinka,"* Zabura 143:10. Manzo Bulus ya yi addu'a cewa masu bi a Kolosiya su *"cika da sanin nufin Allah,"* Kolosiyawa 1:9. Addu'arka ta gaskiya domin kanka da sauran mutane ya kamata ta zama sanin nufin Uba Maiduka da aikata shi.

**Ka sami jagora.** Uba Maiduka yana bayyana nufinsa na musamman ta wurin Kalmarsa, hikimarsa, mutanensa, da salamar da yake bayarwa. Ka roƙi Uba Maiduka ya bayyana maka nufinsa. Zai amsa addu'o'inka ta wurin:

1. Kalmarsa. Sanin nufin Uba Maiduka na musamman sakamakon nazarin Littafi Mai Tsarki a kai a kai ne. Nufin Uba Maiduka a gare ka yana ƙara bayyana yayin da kake samun hikima da fahimta daga Kalmarsa. Ba zai taɓa jagorance ka ka yi wani abu da ya saɓa wa Kalmarsa ba.

2. Hikimarsa. Hikimar Uba Maiduka tana zuwa daga biyayya ta ruhaniya, 1 Korintiyawa 2:14-15. *"Kada ku biye wa zamanin nan, amma ku bar halinku ya sāke, ta wurin sabunta hankalinku ɗungum, don ku tabbatar da abin da Uba Maiduka yake so, wato nufinsa kyakkyawa, abin karɓa, cikakke kuma,"* Romawa 12:2. Ka roƙi Uba Maiduka hikimarsa, *"In waninku ya rasa hikima, sai ya roki Allah ... sai kuwa a ba shi,"* Yakubu 1:5.

3. Mutanensa. Mutanen Uba Maiduka hanya ce ta samun taimako wajen fahimtar nufin Uba Maiduka. Waɗanda suke koyar da Kalmarsa daidai ta magana ko rubutu za su iya taimakawa, Kolosiyawa 1:28. Yana da kyau ka nemi shawara daga manyan masu bi da suka manyanta. Fiye da mai ba da shawara ɗaya abu ne mai kyau, *"Ka nemi dukan shawarwarin da ka iya ka samu, za ka yi nasara, idan ba tare da shawara ba, za ka fāɗi,"* Karin Magana 15:22. Manyan masu bi ba su da cikakkiyar rashin kuskure, amma za su iya ba ka haske mai amfani domin ya taimaka maka ka gane nufin Uba Maiduka.

4. Salamarsa. Salamar Uba Maiduka ita ce tabbatarwa ta ƙarshe ga nufinsa na musamman, *"Salamar Almasihu kuma tă mallaki zuciyarku,"* Kolosiyawa 3:15. *"Ta haka salamar Allah, wadda ta fi gaban dukkan fahimta, za ta tsai da zukatanku da tunaninku ga Almasihu Yesu,"* Filibbiyawa 4:7. Wannan salamar ita ce zurfin tabbaci daga Uba Maiduka cewa shawara ta dace bayan addu'a, nazarin Littafi Mai Tsarki, hikimar ruhaniya, da shawarwari daga masu ba da shawara da suka manyanta a ruhaniya. Ka nemi salamarsa, ka kuma jira ta.

**Ka aikata.** Sa'ad da kake tambaya ko wani abu nufinsa ne, amsar na iya zama "a'a" kamar yadda ta kasance ga Bulus, 2 Korintiyawa 12:7-10. Tana iya zama "ka jira." Amsarsa ta "ka jira" na iya kawo babbar albarka, Ishaya 40:31. Sa'ad da amsar Uba Maiduka ta zama "eh," ka aikata nufinsa ko da yana da wuya, ba ya samun karɓuwa, ko yana da tsada. Ya kamata mu ji daɗin aikata nufinsa daga zukatanmu, Zabura 40:8, Afisawa 6:5-6. Ka yi hankali da amsoshin ƙarya da ake koyarwa da sunan Kiristanci. Ka yi biyayya sa'ad da ka tabbata ka san nufin Uba Maiduka.

---

*Ta Yaya Zan San Nufin Uba Maiduka?* © 2026 na John D. Morris III, Acts One Eight ne suka wallafa. Za ka iya bugawa, kwafa, ɗorawa a yanar gizo, aikawa ta imel, ko aika saƙo da shi kyauta muddin ba a canja abin da ke ciki ba, kuma an haɗa wannan cikakken bayani. Za ka iya ƙara sunan ma'aikatarka ko cocinka ko tambarinka a saman shafi na ɗaya, ka kuma ƙara bayanan tuntuɓarka a saman layin da ke kusa da ƙarshen shafi na biyu. WillofGod316.org yana bisa Littafi Mai Tsarki kaɗai. Yana nan domin ya taimaka wa masu bi su gano nufin Uba Maiduka. Za ka iya aika imel zuwa Acts One Eight (da Turanci idan zai yiwu) zuwa: Hello@Mail316.org. An samar da sabis na fassara ta www.ChristianLingua.com. *Ta Yaya Zan San Nufin Uba Maiduka?* yana samuwa kyauta a harsuna arba'in da takwas a www.WillofGod316.org. An ɗauko ayoyin Littafi Mai Tsarki a sigar Turanci daga New American Standard Bible 1995 na The Lockman Foundation. An ɗauko ayoyin Littafi Mai Tsarki a wannan fassarar daga Littafi Mai Tsarki (Sabon Juyi).